# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na bakwai: Yaƙi halak yaƙi haram

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Sa’adatu: | ’yar shekara 35 |
| Malam Talle: | ɗan shekara 60 |
| Matar M Talle: | ’yar shekara 55 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurare, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu". A yau mun shigo cikin kashi na bakwai na shirin wasan kwaikwaiyonmu mai taken "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". Sai ku gyara zama domin jin yadda za ta kasance a cikin shirin na yau mai taken "Yaƙi Halak Yaƙi Haram". Za mu fara ne daga inda Lami da Sa'adatu suka yi za su haɗu, wato a bakin wani kanti inda za a saya wa Lami kayan sanyi.

**Fitowa ta 1: Lami da Sa'adatu a ƙofar wani kanti**

**Lami:** Wallahi Sa'a, ni na rasa ma bakin magana. Na gode da kika samu damar fitowa, duk da cewa a gurguje na kira ki. Gaskiya kirkin naki ya wuce misali. Wallahi ni dai na kusa fita daga hayyacina. Babu abin da nake yi, daga karatu sai karatu. Duk zaman kaɗaici ya ishe ni.

**Sa'adatu:** Haba Lami, kar ki damu! Ai ya kamata a ce kina ɗan shaƙatawa. Kin fa san rai dangin goro ne, sai da hutu. To, mu shiga cikin kantin mana.

**Lami:** Tabɗi! Lallai wurin nan ba dama ne. Ki duba yadda aka haɗa kantuna dabam-dabam a cikin irin wannan ƙaton ginin. Ga kuma komai gwanin ban sha'awa... Waɗannan nan fa su ne irin kayayyakin da mukan gani a cikin mujalla, ko ba su ba ne?

**Sa'adatu:** Kai, wallahi ke ma dai da abin dariya kike. Ke dai mu je ki ga yadda za ki dawo baƙar Baturiya.

**Lami:** Ni ko don Allah Sa'adatu bari na yi miki wata tambaya. Amma fa kar ki ga na fiye shisshigi.

**Sa'adatu:** Haba, ba komai wallahi, ki yi tambayarki!

**Lami:** Ke kuwa yaya aka yi kika samu kanki a nan Turai? Karatu ne ya kawo ki ko kuwa aiki? Gani na yi komai naki yana tafiya daidai-wa-daida. Ina ma dai ni ce ke!

**Sa'adatu:** To Lami, da farko dai ina so ki gane cewa ba a tambayar ɗan gudun hijira, musamman ma dai daga Afirka, yadda ya samu kansa a Turai. Babu kyau yin hakan. Kuma ki daina cewa da ke ce ni. Ke ma za ki iya mallakar duk abin da na mallaka. Abin da kike buƙata kawai shi ne haƙuri da kuma sadaukar da kai.

**Lami:** Au, haka abin yake? Kina nufin ni ma zan iya samun mota da tufafi da kuma irin gwala-gwalan da kike sawa. Ai kuwa idan haka ne, ya kamata a ce ni ma ina da aiki irin naki!

**Sa'adatu** Mhm, to, kusan hakan. Amma fa ki sani cewa shekarunki ba su kai yin hakan ba. Yanzu dai mu manta da wannan zancen.

**Lami:** Shekaruna ba su kai ba? To idan haka ne yaya aka yi har ma na zo nan Turai. Na fa kusa cika shekara ashirin. Ni gani nake shekaruna sun kai na san ciwon kaina. Kuma kin ce sai na sadaukar da kai, to kamar yaya?

**Sa'adatu:** Tsaya ki ji Lami, mutane fa gani suke a ƙasashen Afirka da kuma Asiyaa da Kudancin Amurka ne kawai ake samun dazuzzuka masu ruƙuƙi. Abin da ba a sani ba shi ne, ita kanta Turai ɗin ma wani dajin ruƙuƙi ne. Bambancin kawai shi ne, Turai daji ne mai cike da gine-gine, amma duk yanayinsu ɗaya ne, duk rayuwar nafsi-nafsi ake yi. Dole ne

mu baƙi mu dinga aiki tuƙuru fiye da ’yan ƙasa, idan har za mu kai labari. … A’a’a, kin ga wata riga! Yaya kika gan ta, ta yi ko ba ta yi ba?

**Lami:** Gaskiya tana da kyau, kuma ta yi. Sai dai kuma…

**Sa’adatu:** Je ki kurum, ki gwada ta mu gani. Idan ta yi, zan biya miki ita.

**Lami:** Gaskiya ke ta dabam ce. Ni ban taɓa yin ƙawa kamarki ba.

**Sa’adatu:** A’a, ba kome!

**Mai ba da labari:**
To, daidai lokacin da Lami take ta jidar kayan sawa, ga iyayenta can an kai musu wani mumman labari. Yanzu bari mu ji irin hirar da suke yi a yayin da suke dawowa gida daga wajen aiki.

**Fitowa ta 2: Mutanen gidan Malam Talle sun dawo daga aiki bayan da aka sallame su daga aiki**

**Malam Talle:** Kai! Don Allah rufe mana baki, wawan kare kawai! Ba ka san halin da muke ciki ba ne?

**Matar M. Talle:** Haba, kai ma dai. Mene ne nasa a sallamar da aka yi mana daga aiki? Kar ka ɗora masa laifi.

**Malam Talle:** Yanzu a ce wai mu shafe shekaru talatin muna aikin gwamnati, shekaru talatin fa ba wasa ba ne! Muna ta yi da ƙarfinmu, amma a rana guda a ce wai an sallame mu daga aiki. Gaskiya Maman Lami, ba a yi mana adalci ba.

**Matar M. Talle:** Ba ka ji ma abin da daraktan namu yake faɗa ba, wai sallamar ruwan dare ce, ta shafi ko'ina a duniya. An ce yanzu sai sallamar mutane ake yi daga aiki a ko'ina. Bari Maigida, kar ka damu, za a san yadda za mu yi.

**Malam Talle:** Ban gane, za a san yadda za a yi ba. Wai me ya sa ne ko da yaushe kura ce ke shan duka gardi na ƙwace kuɗi? Gaskiya ba a yi mana adalci ba. Bari ki ji, Maman Lami, ya kamata a ce an kyautata mana maimakon koranmu.

**Matar M. Talle:** Na san har yanzu ranka a ɓace yake, Maigida, amma bari na ɗan dafa maka shayi mai ɗan zafi ka sha, na san yanzu ka wattsake.

**Malam Talle:** Ke, ni ba shayi ne a gabana ba. Ke yanzu a ganinki shayi ne zai sa na fita daga cikin halin da nake ciki? Ni aikina kawai na damu a dawo min da shi!

**Matar M. Talle:** Tsaya ka ji Maigida, na san halin da ka shiga, kuma ni ma in ce halin da nake ciki. Amma kuma wannan ba zai sa ka dinga fushi da ni ko da wannan karen ba. Ya kamata mu tsaya mu nemi mafita. Kana ganin na faɗa wa Lami halin da muke ciki, ko kuwa?

**Malam Talle:** Ke Tabawa, kanki ɗaya kuwa? Me za ki faɗa mata? So kike ki ce mata yanzu iyayenta ba sa aiki, kuma ba da daɗewa ba za a kore su daga gidan da suke ciki?

**Matar M. Talle:** Maigida, ni sai gani nake kamar ba a hayyacinka kake ba. Lami fa 'yarmu ce ta cikinmu, kuma ita ke nan muke da ita kamar rai. Dole ne ta san halin da muke ciki a gida. Yanzu ba za a iya gaya mata ba tun da yanzu ta mallaki hankalin

kanta, wataƙila ma ta ɗan taimaka mana da wani abu.

**Malam Talle:** Ta taimaka mana? Ta yaya?

**Matar M. Talle:** Da kuɗi mana. Domin na ji an ce yawancin ɗaliban Afirka da ke zaune a Turai kan samu ayyukan yi a lokacin da suka sami hutu. Na san ita ma Lami za ta dinga yin haka. Ka san fa tabbas za mu buƙaci tallafin kuɗi tun da yanzu ba mu da albashi, kuma ga shi mun kashe duk kuɗin da muka adana saboda karatunta.

**Malam Talle:** Mhm. Wato kina nufin ta dinga karatu kuma tana yin aiki ke nan?

**Matar M. Talle:** Kwarai kuwa. Haka nake nufi mana.

**Malam Talle:** Na san haka kike nufi. Amma me ya sa ba ki faɗa mata ba tun da farko? Kina ganin kuwa Lami za ta iya yin haka?

**Matar M. Talle:** Idan ma ba ta san da haka ba kafin ta tafi, yanzu na tabbata ta sani.

**Malam Talle:** Kin fi ni gaskiya fa. Kin ga kuma da ma ita Lami gwanar girki ce. Lallai kuwa Maman Lami, ina ganin kofin shayin nan da kika ce za ki dafa min yanzu zai samu shiga.

**Matar M. Talle:** Ai ka san mu mata akwai mu da 'yan dabaru. Ɗan jira ni kaɗan, ina zuwa.

**Mai ba da labari:**

Da za ka tambayi abin da ke damun duk wani wanda aka sallame shi daga aiki, da zai faɗa maka cewa, baya ga matsalar kuɗi da yake fuskanta, har da

ma kuma ta rashin kwanciyar hankali.
Bari mu koma cikin kantin nan na sayar da kayayyaki, ga Sa'adatu can ta biya kuɗin kayan da Lami ta saya. Ga su can kuma suna cin abinci a wani gidan cin abinci.

**Fitowa ta 3: Lami da Sa'adatu a gidan cin abinci**

| | |
|---|---|
| **Lami:** | Gaskiya wannan kazar ta soyu. Kin san Allah, Sa'a, ban taɓa jin daɗi kamar yau ba tun da na zo Turai. Ai ni yanzu komai ta kama zan yi don ni ma na dinga rayuwa kamar yadda kike yi. |
| **Sa'adatu:** | Kin tabbata kuwa Lami? Kin san fa duk abin da kika zaɓa, ba ja da baya. |
| **Lami:** | Haba, in dai zan dinga samun riguna, da takalma, da kayan sanyi masu kyau, ga kuma abinci mai daɗi, to wane baki biyu kuma zan yi. Ni yanzu dai kawai gaya min abin yi. |
| **Sa'adatu:** | Tsaya tukun, yaya maganar saurayinki? |
| **Lami:** | Wa ke nan? Me kike nufi? |
| **Sa'adatu:** | Shi ɗin dai nake nufi. A wane matsayi kika sa shi a rayuwarki? |
| **Lami:** | E to, har yanzu ina ƙaunansa, amma fa dole na yi tunanin irin rayuwar da nake yi a nan Turai. Shi ma kuma na san yana can yana tsarin irin rayuwarsa a can gida. |
| **Sa'adatu:** | Ba kun shirya yin aure ba? |

**Lami:** Gaskiya mun shirya, amma fa sai na kammala karatuna. Amma a halin yanzu, zan miƙe ƙafata ne na more rayuwata kamar yadda sauran ɗalibai ke yi.

**Sa'adatu:** Don Allah Lami, za ki iya riƙe min wani sirri?

**Lami:** Zan iya mana.

**Sa'adatu:** Ina fa nufin sirri na sosai. Kuma ba na son kowa ya ji, duk yadda kuke da shi.

**Lami:** Har da iyayena?

**Sa'adatu:** Har iyayen naki, har ma da…

**Lami:** To, shi ke nan, sai dai kawai na fara jin wani iri fa. Wai ma sirrin na mene ne? Kar dai ki ce min kina hulɗar miyagun ƙwayoyi ne?

**Sa'adatu:** Wallahi sam! Ba haka ba ne. Ke yanzu kin ga na yi kama da masu hulɗa da miyagun ƙwayoyi?

**Lami:** Ba haka ba ne. Tun kafin na zo nan ne, sai da aka ja min kunne cewa harkar miyagun ƙwayoyi na ɗaya daga cikin matsalolin da ake fuskanta a nan Turai. Kuma an ce akwai ma wasu da ke wannan harkar a cikin jami'ar da nake karatu.

**Sa'adatu:** To, gaskiya zan gaya miki Lami. Ni ba na shan miyagun ƙwayoyi, kuma ba na kasuwancinsu.

**Lami:** To, idan haka ne, mene ne sirrin naki? Ko dai kina

karuwanci ne?

**Sa'adatu:** Mmm, yanzu idan na ce miki, e, me za ki ce?

**Lami:** Abin da zan ce shi ne: "Sa'adatu na ji daɗin haɗuwa da ke. Kuma na gode da irin yadda kika ba ni lokacinki. Amma kuma sai dai ki yi haƙuri, ni ban zo Turai don na sayar da mutuncina saboda kuɗi ba."

**Sa'adatu** Da gaske haka za ki faɗa min?

**Lami:** Kwarai kuwa. Ni akwai irin abubuwan da zan iya yarda da su a rayuwata, amma kuma akwai waɗanda sam ba zan yarda da su ba, saboda sun saɓa da tsarina. Karuwanci na ɗaya daga cikin abin da ba zan taɓa yi ba a rayuwata.

**Sa'adatu** Kar fa ki manta kin ce za ki iya riƙe min sirri. Ko ba haka ba?

**Lami:** Gaskiya ne zan iya, matuƙar ba zai cutar da ni ko waɗanda nake ƙauna ba.

**Sa'adatu** To, na ji. Amma Lami, ɗazu-ɗazun nan kika ce kina sha'awar yin rayuwa irin tawa ko? Kuma kin ce kina nan a shirye ki yi ko ma mene ne ko? To bari in gaya miki yadda harkar take.

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, ko kuna son jin irin harkar da Sa'adatu za ta gaya wa Lami, da kuma irin amsar da ita Lamin za ta bayar? Haka kuma kuna son jin irin halin da abokanmu na Arewacin Afirka suke ciki, wato Faisal da Suleman? Don jin yadda za ta kasance, sai ku saurari kashi na gaba na wasan

kwaikwayonmu mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai”. Kuma kuna iya tuntuɓarmu ta yanar gizo a shafinmu na Facebook, wato: facebook.com/dw.lbe don tattaunawa a kan wannan batu, da kuma irin abubuwan da ya kamata ’yan gudun hijira su dinga yi kafin a ba su damar zama a Turai. Kafin nan sai mu ce, ku huta lafiya.